
محمد

# MANZON ALLAH ANNABI MUHAMMAD

(Sallallahu Alaihi Wasallam)

KAMAR GAKA GA SHI

NA

Abubakar Abbas

1434=2013

# GABATARWA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talifiai. Tsira da aminci su tabbata ga Annabi Muhammad fiyayyen Annabawa da Manzanni, da iyalansa da dukkanin mabiyansa har zuwa ranar sakamako.

Bayan haka, kasancewar Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) shi ne wanda Musulmai suke da kyakkyawan abin koyi tattare da rayuwarsa, na gaya dace in gabatarwa da 'yan uwa Musulmai wannan littafi mai ɗauke da bayanin kyawawan siffofinsa don samun abin kwaikwayo a gare mu.

A fiarshe, ina rofion Allah ya karɓa mini, kuma ya amfani Musulunci da Musulmai da wannan littafi, amin.


Ɗan uwanku a Musulunci,

Abubakar Abbas

Kano – Nijeriya

08035945930



Buga na Biyu

1434= 201

## SUNAYEN MANZO ( Sallallahu Alaihi Wasallam)

Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yace: “ina da sunaye biyar; ni ne Muhammad, kuma ni ne Ahmad, kuma ni ne Mahii, wanda Allah yake shafe kafirci da ni, kuma ni ne Hashiru, wanda za a tashi sauran mutane ina kan kafafuwana, kuma ni ne Afiibu, wanda babu wani Annabi bayansa”. ( Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi).

## SIFFOFIN MANZO (Sallallahu Alaihi Wasallam)

Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya kasance mai kyan jiki ne, ba mai fiiba ba ne, kuma ba siriri ba ne, ba dogo bane, kuma ba gajere ba ne, fari ne shi, kai kace da azurfa aka yi shi, mai tajajjen gashi ne, mai yawan gemu ne, mai yalwar kai ne da hannaye da kafafuwa.

Kuma Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi mai kyakkyawar fuska ne, kamar rana da wata, kuma fuskarsa kewaye take, kuma yana da faɗin kafaɗu. Ga shi kuma da daɗin fianshi.

## ZANCEN MANZO (Sallallahu Alaihi Wasallam)

Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, mai yawan shiru ne, kuma idan zai yi Magana baya fadar son zuciya. Allah Maɗaukaki yace:

---

1

Saboda fianshin jikin Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) har ma sahabbai sukan tari guminsa a kwalaba, domin shafawa a tufafinsu idan sun yi kwalliya.

“Manzo baya faɗar son zuciya”

Kuma baya faɗar wata Magana sai gaskiya, zancensa a bayyane yake daki-daki, yadda duk wanda ya zauna ya saurare shi zai iya haddace shi, kuma ya kasance yakan maimaita kalma sau uku don a fahimce shi, kuma idan Manzon Allah tsira da amincin Allah tabbata a gare Shi ya yi Magana wanda yake ido biyu zai ji shi, kuma mai barci ba zai farka saboda maganarsa, ba kari akan haka, Allah yaba shi kalmomi masu tarin bayanai.

Surar Najmi,aya ta 3.

KARATUN MANZO (Sallallahu Alaihi Wasallam)

Allah Maɗaukaki yace da Manzonsa (Sallallahu Alaihi Wasallam):

“ka kyautata karatun Alkur’ani matukar kyautatawa”

---

1

Suratul Muzammil, aya ta 4.

Sai Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya kasance yana yan-yanka karatunsa, aya-aya, yana cewa: (Alhamdulillahi rabbil alamin)

Sannan ya tsaya, sannan yace: (Arrahamanurrahim)

Sannanan ya tsaya, kuma yana jan muryarsa da karatu ja sosai. Sannan kuma karatunsa, tsira da amincin Allah su tabbata agareshi, karatu ne daza A iya fassara shi harafi harafi.

Suratul Fatiha, aya ta (1-2)

KUKAN MANZO (Sallallahu Alaihi Wasallam)

Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata agareshi ya kasance yana kuka a cikin salla don tsoron Allah, kuma yana kuka yayin sauraron karatun Alfiur’ani daga waninsa, kamar Abdullahi ɗan Mas’ud,Allah ya yarda dashi. Kuma Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi yana kuka don tausayin wani abu, kamar yadda yayi kuka don tausayin rasa ɗansa Ibrahim da rasa jikarsa wacce ‘yarsa Zainab ta Haifa.

Kuma kukan Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata agareshi, shi ne idanuwansa suyi hawaye, su kuma zubar ba hawayen, idan kuwa kukansa ya tsananta sai aji yana shasshefia kamar yanayin tafasar tukunya, kuma Manzo tsira da amincin Allah su tabbata agare shi baya kwarma ihu ata dalilin kuka.

DARIYAR MANZO (Sallallahu Alaihi Wasallam)

Mafi yawancin dariyar manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata agare shi murmushice, kuma dariyarsa kaɗance , matukar dariyarsa fifiofiinsa su baiyana, sam sam bai taɓa yin dariyar daza aga cikin bakinsa ba, abin nufi baya fiyalfiyala dariya

CIN ABINCIN MANZO (Sallallahu Alaihi Wasallam)

Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi baya kushe wani abinci.

Idan yayi sha’awar abinci yaci, idan kuma baya sha’awarsa ya bar shi. Kuma yana ambaton Allah Maɗaukaki a farkon cin abincinsa yana mai cewa: bismillahi don kada shaiɗan yaci masa abinci.

Kuma yana godewa Allah a fiarshen cin abincisa sai yace: alhamdulillahi. Sannan kuma Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata agareshi baya cin wani abu a kishingiɗe.

Kuma ya kasance yana amfani da damansa don cin abincinsa, kuma yana cin gabansa ne, kuma idan lomarsa ta faɗi fiasa yana ɗauka yaci bayan cire inda fiasa ta taɓa. Sannan kuma yana ci ne da yatsu uku, yana kuma suɗe yatsunsa da kwanon cin abincinsa idan ya gama.

SHAN MANZO (Sallallahu Alaihi Wasallam)

Mafi yawancin shan Manzo a zaune ne, kuma yana sha a tsaye saboda wani uzuri.

Kuma yana ambaton Allah a farkon shan nasa, ya kuma gode masa a fiarshe.

Sannanan kuma yana numfashi ne a wajen abin shansa sau uku, kuma idan Manzo tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya gama shan abu, sai ya mifiawa wanda yake damansa.

TAFIYAR MANZO (Sallallahu Alaihi Wasallam)

Tafiyar Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi tsaka-tsaki ce. Da ganin tafiyarsa za a san shi ba gajiyayye ba ne. kuma ba malalaci ba ne. kuma sam sam baya tafiyar fiasaita saboda yasan Allah baya sonta. Kuma baya waiwaye idan yana tafiya.

Kuma idan yana tafe tare da sahabbansa, sukan zamo a gabansa ne, su barwa Mala'iku bayansa.

RUFEWA SALATIN MANZO (Sallallahu Alaihi Wasallam)

Allahumma salli ala Muhammad wa ala ali Muhammad kama sallaita ala Ibrahim wa ala ali Ibrahim wa barik ala Muhammad wa ala ali Muhammad kama barakta ala Ibrahim wa ala ali Ibrahim fil alamina innaka hamidun majid.